


Aliyah bebiya ce.
Ba ta da abokan wasa.
Aliyah tana da kule.
Kulen ce abokiyar wasanta.


Wata rana Aliyah na bin
kule da gudu.
Sai Aliyah ta yi karo da
wata yarinya.
Aliyah ta faɗi.
Yarinya ma ta faɗi.



Sunan yarinyar Tala.
Aliyah na magana da hannu.
Tala na magana da hannu.
Tala ma bebiya ce.





Aliyah da Tala sun manta da faɗuwa.
Suna ta dariya.
Suna murna karo da juna.



Aliyah ta sami abokiyar wasa.
Tala ta sami abokiyar wasa.



Aliyah ta sami abokiyar hira.
Tala ta sami abokiyar hira.

Kulen Aliyah ma ta samu abokiya.
Kule ne wasa da Aliyah.
Kule na wasa da Tala.